***Maraba da zuwa nazarinmu na Littafi mai Tsarki. Ayau, zamu yi karatun wani yar littafi ce da aka lakaba mata suna "Babu mutumin da ya san ranar ko sa'ar?" Wannan yar littafi ta samar da shaidu daga Littafi mai Tsarki da cewa ranar shari'a zai kasance akan ranar 21 ga Mayu, shekara ta 2011.***

# BABU MUTUMIN DA YA SAN RANAR KO SA'AR?

Babu wani sai dai Allah wanda ya san lokacin karshen duniya. Ta yaya wani zai yi yunkurin koyarwa da cewa fyaucewa da ranar shari'a zasu auku akan ranar 21 ga Mayu, 2011? Ko Littafi mai Tsarki bai ce a sarari da cewa babu wanda zai iya sani ranar ko sa'ar dawowar Almasihu ba? Lallai kam, Littafi mai Tsarki ya koyar da wannan. Littafi mai Tsarki ya nuna ko me ya sa ya koyar da wannan. Cikin littafin Ayyukan Manzanni sura ta farko a aya ta 7, a lokacin da lokacin tazarar ikkilisiya na sabuwar alkawari na dab da farawa, Yesu ya koya wa almajiransa:

***"Ya ce masu, ba naku bane da za ku san zamanin da wokatai wadanda Uba ya sanya a cikin nasa hukunci."***

Sa'annan Yesu ya ce a aya a gaba:

***"Amma za ku karbi iko lokacin da Ruhu mai Tsarki ya zo bisanku; za ku zama shaiduna kuma cikin Urushalima a cikin dukan Yahudiya da Samariya har kuma iyakan duniya."***

Daga wadannan ayoyin mun koya cewa cikin lokacin tazarar ikkilisiya za a sami tambayoyi da dama game da lokacin karshe, amma bai kamata masu bi su bar wannan tambayar ya kwashe hankulansu ba sai dai su dukufa su kuma mayar da hankalinsu ga hidimar kawo bishara zuwa ga dukan duniya.



Sabili da wannan, ko da yaya ne ilimin wani yake, kome horaswan wani malamin tauhidi ko dalibin Littafi mai Tsarki, komin luransa cikin nazarinsa na Littafi mai Tsarki ko kuma bautar Almasihun sa, abu mara yiwuwa ne a koya daga Littafi mai Tsarki shirin lokuta domin karshen duniya. Duk wanda ya yi kirarin cewa ya san lokacin karshen a kullum ba daidai ya ke ba.

Ko da ya ke, akwai wani magana mai daukan hankali a cikin Littafi mai Tsarki. An rubuta wannan cikin littafin Mai-Wa'azi sura 8 a aya ta 5. Acan kuwa Allah ya ce:

***"Dukan wanda ya ke bin doka ba za'a cuce shi ba, zuciyar mai-hikima kuwa ta kan gane kwanaki da shari'a kuma."***

Cikin Littafi mai Tsarki mai-hikima mai bi ne na gaske, wanda Allah ya ba shi kyakyawar yarda cikin hukumar Littafi mai Tsarki. Masu na gaske sun yi ta kasancewa tun farkon lokaci. Amma jerin lokuta cikin tarihi kamar yadda yake cikin Littafi mai Tsarki ba a taba bayyana shi ga zukatan masu bi na gaske ba. Alal misali, duk cikin yawancin lokacin tazarar ikkilisiya an gaskata gaba daya cewa hallita ya auku ne cikin shekara ta 4004 kafin zuwan Almasihu.

Ko da ya ke, kimanin shekaru 35 da suka wuce Allah ya fara bude fahimtan masu bi na gaske ga jerin lokuta cikin tarihi. Don haka, an gano cewa Littafi mai Tsarki ya koyar da cewa idan an gwada abubuwan da sun faru ada da kalandar mu na zamani, zamu iya yin koyi da kwanaki cikin tarihi kamar su hallita (11,013 kafin zuwan Almasihu), da ruwan tufanan kwanakin Nuhu (4990 kafin zuwan Almasihu), da fitowar Israila daga Masar (1447 kafin zuwan Almasihu) da kuma mutuwar Sulaimanu (931 kafin zuwan Almasihu).*

Ko da ya ke, Allah bai bar cikakiyar sani, daga Littafi mai Tsarki ga masu bi na gaske ba game da dukan jerin lokuta cikin tarihi sai bayan yan shekaru da suka wuce. Wannan jerin lokutan ya mike har zuwa karshen lokaci. Cikin wadannan yan shekaru da sun wuce Allah yana ta bayyana gaskiya masu yawan gaske, wadanda ada an boye su gaba daya cikin Littafi mai Tsarki sai zuwa wannan lokaci da muna dab da karshen duniya.

---

Dubi "Adamu, Tun Yaushe?" wato "Adam When?" a turance bugu na farko cikin 1974. Ana iya samu littafin cikin turanci kyauta daga Family Radio, Oakland, CA, 94621, USA, ko kuma za a iya saukewa daga addareshin mu akan yanar gizo, wato www.familyradio.com.



**Ta yaya wannan ya ke faruwa?**

An yi annabcin faruwa wannan a sarari a cikin Littafi mai Tsarki. Littafi mai Tsarki shi ne kalma mai-rai da yake bidan Ruhu mai Tsarki ya bude fahimin mutumin da yake karatu ko saurarон kalaman Littafi mai Tsarki cikin ruhaniya. Don haka, tun da ba nufin Allah ba ne ya bude fahimin wani ga dubbi gaskiyan nan daga Littafi mai Tsarki sai dab da lokacin karshen duniya, sai yanzu ne kadai wadannan gaskiyan cikin Littafi mai Tsarki masu muhimmanci matuka ake iya fahimtansu. Littafi mai Tsarki ya gaya mana cewa wannan zai faru.

**LITTAFIN DA AKA HATIMCE**

Cikin littafin Daniyel Allah yana da abubuwan fadi da dama game da batutuwan karshen lokaci. Daniyel ya fahimce da damansu, kuma domin munin wadannan sakonan, Daniyel ya sha azaba dayawa. Mun karanta wannan, alal misali, cikin Daniyel sura 8 a aya ta 27:

***"Sai ni Daniyel na suma, na yi ciwo kuma yan kwanaki, sa'annan na tashi, na yi ta sha'anin sarki: Na yi mamaki da ru'yan, amma babu wanda ya gane ta."***

Amma kuma Allah ya gaya wa Daniyel cikin Daniyel sura 12 a aya ta 4 da ta 9 da cewa:

***"Amma kai, ya Daniyel, ka kulle zantattukan, ka rufe littafin da hatimi, har kwanakin karshe, mutanne da yawa zasu kai da kawo a guje, ilimi kuma za ya karu. Ya ce, yi tafiyarka, ya Daniyel, gama an kulle zantattukan, an hatimce su har kwanakin karshe."***

A wasu kalamai, Allah yana gaya mana cewa akwai muhimmiyar sako game da lokacin karshe da aka rubuta a cikin Littafi mai Tsarki ('littafin"), amma Allah ba zai bayyana ta ba sai dai karshe duniya ya kusa.

Cikin Ruya ta Yohanna sura 22 a aya ta 18 zuwa ta 19 mun karanta cewa:

***"Ina shaida wa kowane mutum wanda yake jin zantattuka na annabci na wannan littafi, idan kowa ya kara wa littafin nan, Allah zai kara masa anobai wadanda aka rubuta cikin wannan littafi. Kuma idan kowa ya dauka wadansu daga cikin zantattukan littafin wannan annabci, Allah za ya kawar da rabonsa daga cikin ita ce na rai, daga cikin birni mai-tsarki kuma, wato daga cikin abin da aka rubuta cikin wannan littafi."***



Wadannan ayoyin sun tabbatar mana sarai da cewa bayan an kamala Littafi mai Tsarki kimanin shekara ta 95, shekarar Ubangijinmu, ba za a taba iya kara wasu kalamai a cikin Littafi mai Tsarki kuma ba. Don haka, ko da wacce sako ne game da karshen lokaci da aka ba wa Daniyel, da kuma ba za a fahimta ba sai zuwa karshen lokaci, dole ya zama Littafi mai Tsarki yana kunshe da ita kafin a kamala rubutun Littafi mai Tsarki. Ko da ya ke, Allah ya rubuta su cikin hanyar da ba za a iya fahimta ba sai dai idan duniya ta yi kusa da karshenta. Tuna dai, fahimi daga wurin Ubangiji Yesu Kristi ya ke zuwa, kamar yadda mun karanta cikin Luka sura 24 a aya ta 45: "Daga nan ya bude hankalinsu, domin su fahimce littatafai." Wannan ya bayyana masababin rubutun Littafi mai Tsarki cikin harshe mai cunkusu, kuma mai wuyan ganewa hakanan. Wannan yana daya daga cikin dalilan da sun sa Almasihu ya yi magana da misalai, kamar ma yadda mun karanta cikin Markus sura 4 a aya ta 34: "kuma ba ya yi masu zance ba sai da misalai."

**AN BUDE LITTAFIN**

Amma kuma mun karanta cikin Ruya ta Yohanna sura 5 a aya ta farko zuwa ta 9 da cewa:

***"A cikin hannun dama na wanda ke zaune bisa kursiyin na ga littafi cike da rubutu a cikinsa da bayansa, an hatimce shi da kyau da hatimi bakwai. Na ga kakarfan malaika kuma yana shelar da murya mai-karfi, wanene ya isa da zai bude littafin, shi kwance hatimansa? Amma ba a samu kowa wanda yake da iko cikin sama, ko a kan duniya, ko karkashin duniya, da za shi bude littafin, ko kuwa shi duba a cikinsa ba. Sai na yi kuka da yawa, da ba a iske kowa wanda ya isa shi bude littafin, ko kuwa shi duba cikinsa ba. Amma daya daga cikin dattiban ya ce mani, kada ka yi kuka, ga shi, zaki wanda yake na asalin kabilar Yahuda, tushen Dawuda, ya rinjaya, da zai bude littafin ya balle hatimansa bakwai. A cikin tsakiyar kursiyin da na masu-ran nan hudu, a cikin tsakiyar dattiban kuma, na ga dan rago a tsaye, kamar an yanka shi, yana da kaho bakwai, da idanu bakwai, ruhohin Allah bakwai ke nan, aikakku cikin dukan duniya. Ya zo, ya amshe shi daga hannu dama na wanda ke zaune a bisa kursiyin. Sa'anda ya amshi littafin, masu-ran nan hudu***

***da dattibai ashirin da hudu suka fadi a gaban dan rago, kowane a cikinsu yana da giraya, da kasake na zinariya cike da turare, wato adduo'in tsarkaka ke nan. Suna raira sabuwar waka, suna cewa, mai-isa ne kai ka dauki littafin, ka balle hatimansa, gama an kashe ka, kuma da jininka ka saye wa Allah mutane daga cikin kowace kabila, da kowane harshe, da al'umma, iri-iri."***

Wadannan ayoyin suna koyarwa da cewa akwai wani littafi da aka hatimce da kuma Almasihu ne da kansa zai bude shi. Littafin kadai da zai iya yiwuwa an kafa mata ido ita ce littafin da Littafi mai Tsarki ya kwatanta cikin Daniyel sura 12: An hatimce wannan litttafin da hatimai bakwai.

Don haka, kafin a sami cikaken fahimtan dukan sakonai da aka rubuta cikin wannan littafin, dole a dauke dukan hatiman nan bakwai. Lallai kam, Ruya ta Yohanna sura 8 a aya ta farko ya kwatanta cirewan hatimin na bakwai:

***"Sa'anda ya bude hatimi na bakwai, sai daga baya aka yi shuru cikin sama wajen rabin sa'a guda."***

**A YAUSHE NE AKA YI SHURU CIKIN SAMA?**

Shekaru da dama da suka wuce mun koya cewa shurun nan a cikin sama da ya dauki kusan rabin sa'a guda yana magana ne kan kwanaki 2,300 da sun kasance sashi na farko na lokacin matsananciyar kunci mai tsawon shekaru 23 (wato daidai kwanaki 8,400). Wannan lokacin ya fara daga ranar 21 ga Mayu, 1988. Cikin wannan lokacin ne mai tsawon kwanaki 2,300 da cikin ikkilisiyai da kuma cikin dukan duniya, kima ne, idan har akwai ke nan, sun sami ceto. Ruya ta Yohanna sura 8 a aya ta farko ya nuna cewa an yi shuru cikin sama. Wannan ne ya kamata ya zama yanayin tun daga ranar 21 ga Mayu 1988, domin ana farinciki a sama akan masu-zunubi da sun tuba. Cikin Luka sura 15 a aya ta 4 zuwa ta 32 Littafi mai Tsarki ya nuna wannan farincikin a sama, farinciki ne da ba shuru ake yi da ita ba.

Mun rigaya mun koya cewa ranar 21 ga Mayu, 1988 ne ya kasance rana ta karshe na lokacin tazarar ikkilisiya ya kuma zama ranar farko na lokacin matsananiyar kunci mai tsawon shekaru 23, wanda a cikin wannan lokaci Allah ya dauko shaitan ya sanya shi mulki akan dukan ikkilisiyai da ma dukan duniya gaba daya. Cikin kwanaki 8,400 Ruhu mai Tsarki ya janye kansa daga dukan ikkilisiyai da ma daga cikin dukan duniya. Wannan



ya kawo shuru cikin sama. Wannan yanayin na bakinciki zai cigaba cikin ikkilisiyai har zuwa karshen lokacin nan na matsananciyar kunci mai tsawon shekaru 23. Ko da ya ke, farawa daga ranar 21 ga Mayu 1988 (wato ranar karshen lokacin tazarar ikkilisiya), an sake zubo da Ruhu mai tsarki kuma, wanda ya haifar da abin da Littafi mai Tsarki ya ce da shi "ruwan karshe" (Zakariya sura 10 a aya ta farko, Yakubu sura 5 a aya ta 7)duk duniya (amma ban da cikin wani ikkilisiya), Allah kuma ya soma shigo da anfanin ceto ta karshe, yana kawo farinciki cikin sama. Wannan ceto ba a cikin ikkilisiya ya ke aukuwa ba, amma zai cigaba gabanai da ikkilisiyai har zuwa karshen matsananciyar kunci, akan ranar 21 ga Mayu, 2011.

Domin a farkon lokacin matsananciyar kunci (ranar 21 ga Mayu, 1988) Almasihu ya dauke hatimi na bakwai wanda shi ne na karshe daga wannan littafi da aka umurce Daniyel ya hatimce, yanzu muna iya fahimtan dalilin da ya sa Allah ga bayyana mana gaskiya da dama daga cikin Littafi Mai Tsarki cikin yan shekarun nan da sun wuce. Wannan na kunshe da daidai lokacin karshe da kuma da dama daga cikin shirin Allah na shari'a. Kalmar nan "lokaci" akan more ta a maimaikon 'sa'a.' Shari'a kuma yana magana akan ranar shari'a ne, wanda an saba ce da shi 'ranar.' Don haka, sani lokaci da shari'a kamar yadda an yi annabci cikin Mai-Wa'azi sura 8 a aya ta 5 ita ce sanin 'ranar' da kuma 'sa'ar.' Wannan yana daidatuwa sarai da jinkai da kuma kaunar Allah domin dukan duniya. Tuna dai, Allah ya bawa Nuhu daidai sakon domin ya iya yi wa duniya kashedi game da hallakaswa da ke zuwa. Haka ma, Allah ya umurce Yunana ya ba wa mutanen Ninevah daidai ranar da ya shirya ya hallakadda birni Ninevah. Haka kuma, cikin jinkansa da kaunarsa Allah ya bawa masu bi na gaske na kwanakin mu daidai lokacin fyaucewa, wanda ita ce ranar farko na ranar shari'a, domin su iya wa duniya kashedi. Duba alherin, da kyaun zuciya da kuma kaunar Allah. Kuma abin mamaki, Allah yana kan ceton mutane da dama ayau (Ruya ta Yohanna sura 7 a aya ta 9 zuwa ta 14) kamar ma yadda ya cece mazaunan Ninevah cikin kwanakin Yunana (Matta sura 12 a aya ta 41).

**BABBAR KASHEDI GA WADANDA SUKE CIKIN IKKILISIYAI.**

Sanin asalin lokacin fyaucewa da kuma fahimtan ranar shari'a yana da matukar muhimmanci. Allah ya bada kashedi cikin Tassalunikawa ta fari sura



5 a aya ta 2 zuwa ta 3 game da zuwan ranar shari'ar domin ya hallaka wadanda sun yi musun cewa muna kusa da karshen duniya. Masu bi na gaske zasu san lokacin (sa'ar) dawowar Almasihu domin ya shigo da masu bi na gaske cikin sama (fyaucewa) a kuma soma ranar shari'a. Acan Allah ya gaya mana cewa:

***"Gama kun san sarai ranar Ubangiji tana zuwa misalin barawo da dare. Bayan suna cikin fadin, kwanciyar rai da lafiya, sai hallaka faraf ta auko masu, kamar yadda nakuda ta kan auko wa mace mai-ciki, ba kuwa za su tsira ba ko kadan."***

Cikin Ruya ta Yohanna sura 16 a aya ta 15 Almasihu ya koyar da cewa shi da kansa, zai zo kamar barawo (duba Ruya ta Yohanna sura 3 a aya ta 3). Almasihu dai ba barawo bane. Shi ne Allah mai-tsarki. Amma shi da ranar shari'a zasu zo kamar barawo. Cikin Yohanna sura 10 a aya ta 10 Allah ya kwatanta abin da barawo ya ke yi idan ya zo: ***"Barawo ba ya kan zo ba sai domin sata, da kisa, da hallaka."***

Saboda haka, lokacin da Almasihu ya zo da ranar shari'a, yana zuwa ne domin ya dauke rai ya kuma hallaka wadanda ya bayyana a garesu kamar barawo. DA DARE NE BARAWO YA KE ZUWA.

Almasihu da ranar shari'a zasu zo da dare ne. Cikin Tassalunikawa ta fari sura 5 a aya ta 3 Almasihu ya gaya mana, "bayan suna cikin fadin kwanciyar rai da lafiya, sa hallaka faraf ta auko masu." Domin hallaka ya auko masu, mu'a iya sani tabbataciya da cewa ba a cece wadannan mutanen ba. Tun da ba'a cece su ba, suna cikin duhu ne cikin ruhaniya. Suna cikin dare. Ranar shari'a yana zuwa masu kamar "barawo da dare." Duk da haka sun gaskata cewa suna nan da kwanciyar rai da Allah kuma lafiyayyu karkashin kulawarsa.

**SU WANENE WADANNAN MUTANEN?**

Harshen wannan aya ya kwatanta da kyau dukan wadanda suke cikin duniya wadanda har akan ranar 21 ga Mayu, 2011 suna kan bin wani ikkilisiya. Domin ikkilisiyai suna koyar da abubuwa da dama da ba gaskiya suke da Littafi mai Tsarki ba, har da shirin ceto da ya saba wa Littafi mai Tsarki, Ruhu mai Tsarki kuma ya yashe dukan ikkilisiyai, wadanda suna kan bin wani ikkilisiya har akan rana ta 21 ga Mayu, 2011 ba a cece su ba. Ko da ya ke ikkilisiya suna koya wa mabiyansu cewa:



1. Su a matsayin mabiya da sun shaida ijirorin ikkilisiyar suna nan a tsare cikin kulawar Almasihu.

2. Babu wanda zai iya sanin ranar ko sa'ar dawowar Almasihu. Don haka, sun tabbata cewa Almasihu zai zo kamar barawo ne da dare.

Wadannan kaunatattu mutane basu gane ko kadan da cewa su da kansu suna cikin dare bane cikin ruhaniya, yanayin da ya tabbatar da cewa idan Almasihu ya dawo, su da kansu, za a hallaka cikin ranar shari'a. Dubi munin wannan! Masu bi na gaske ne sun san lokacin (sa'ar) sun kuma san abubuwa sosai game da ranar shari'a (ranar). Ba cikin duhun daren na ruhaniya suke ba.

A TUNA, Allah mai jinkai ne sosai kuma wai kauna ne. Akwai bege ga kowannen da ya yi kuka da duk kaskanci, ya roka, ya bidi Allah cewa watakila shi ma, watakila ya sami ceto.

Domin karin koyi game da bayyanai na karshen duniya ana gayatan ka ka rubuta wa Family Radio cewa kana neman wadannan littafan da suke kyauta, ko ka dubi littafan akan addareshinmu akan yanar gizo. Suna samuwa cikin harshe turanci da harshen Spanish, da harshen Faransa da ta Sin (Chinese), da kuma cikin wasu harsuna da dama.

Littatafai: **"Muna Dab Da Can"** wato "We Are Almost There."
**"Daukaka ya Tabbata ga Allah"** wato "To God be the Glory."
**"Ina Fata Allah zai Cece Ni"** wato "I Hope God Will Save Me."

Kankananan littatafai:
**"Ranar Shari'a: 21 ga Mayu, 2011"** wato "Judgment Day: May 21, 2011."
**"Alla ya Bada Wani Shaida..."** wato "Another Infallible Proof..."

Wannan ya kamala karatun mu na wannan yar littafin. Allah ya sa cikin addu'a ka dubi abin da Allah zai yi da rayuwarka cikin kankanin lokacin nan da ya yi saura wa duniyan nan duban abin da ka saurara ayau.

Yanar gizo: **http://www.familyradio.com**

Addareshi akan gizo:
**international@familyradio.com**

Addareshi gidan-waya:
**Family Stations, Inc.,**
**Oakland, California, 94621, USA.**

NO MAN KNOWS/HAUSA 06-29-'10